# Bauta da Allah Ya Amince da Ita (Sashe na 2)

An ɗauko daga babi na 15 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?* za a iya samunsa a dandalin jw.org/ha.

**MANUFA: Ka bincika abin da ka yi imani da shi da kuma dalilin da ya sa ka yi hakan, kuma ka bincika abin da Littafi Mai Tsarki ya koyar don ka iya bayyana ma wasu abin da ka yi imani da shi.**



## IDAN MUKA GASKATA CEWA ALLAH YA WANZU, HAKAN NE KAƊAI ZAI WADATAR?

### 1 KA BINCIKA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

Me ya sa wasu mutane za su ce e?

Me ya sa wasu mutane za su ce a'a?

Me *ka* yi imani da shi?

Me ya sa ka yi imani da hakan?



www.jw.org/ha © 2016 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## 2 KA BINCIKA ABIN DA LITTAFI MAI TSARKI YAKE KOYARWA

### Wajibi ne mu bauta wa Allah a hanyar da yake so.

(Ka duba babi na 15, sakin layi na 15-18 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

**Karanta Yaƙub 2:19.**

Ta yaya ayar nan ta nuna cewa ba gaskata cewa Allah ya wanzu ne kaɗai zai wadatar ba?

**Karanta 2 Korintiyawa 6:17.**

Idan muna so Allah ya 'karɓe mu,' ko kuma ya amince da mu, mene ne ya kamata mu yi idan ya zo batun ibadar da ba ya so?



**Yi wa Allah sujjada tare da bayinsa zai sa mu sami albarka mai yawa**



www.jw.org/ha © 2016 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

**Idan muna bauta wa Jehobah tare da mutanen da ya amince da su, za mu sami albarka, kuma abin da za mu samu zai fi abin da muka sadaukar.**
(Ka duba babi na 15, sakin layi na 19-20 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

## Karanta Markus 10:28-30.

Bisa ga abin da Yesu ya faɗa, wane albarka ne mabiyan Yesu za su samu a yanzu da kuma a nan gaba?

___

___

___

___

## Karanta 2 Bitrus 3:9, 13.

Mene ne ya sa ya kamata mu yi iya ƙoƙarinmu don mu bauta wa Allah a hanyar da yake so?

___

___

___

___

Wane albarka ne ka samu don kana bauta wa Allah tare da bayinsa?

___

___

___

___


www.jw.org/ha © 2016 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## 3 KA BAYYANA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

IDAN WANI YA CE…

**Muddin ka gaskata da Allah, abin da ya fi muhimmanci ke nan.**

ZA KA IYA CE…

**Gaskiya ne cewa yana da muhimmanci mu ba da gaskiya cewa Allah ya wanzu. Amma na san cewa muna bukatar mu yi fiye da ba da gaskiya kawai domin…**

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?

IDAN WANI YA CE…

**Ba sai ka zama mamban wani addini kafin ka faranta wa Allah rai ba.**

ZA KA IYA CE…

**Mutane da yawa za su yarda da kai. Amma abin da na gaskata ya bambanta da ra'ayinka domin…**

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?


www.jw.org/ha © 2016 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania